# Surah 111: Al-Masad - سورة المسد

بسم الله الرحمن الرحيم
[111:0] Bismi ***ALLAH***, Alrahman, Alrahim.

تَبَّتۡ يَدَآ أَبِي لَهَبٖ وَتَبَّ ١

[111:1] Hannaye biyu na Abulahabi sun halaka, kuma ya halaka.

**111:1 Abu Lahabi, da shi kawun Muhammad ne, kuma shugaban masu adawa da shi. Matarsa ce ta yi yaqin neman a gallaza wa Muhammad da wadansu mu'minai. Kamar duka misalan da akan yi na siffanta Aljannah da Jahahannamah, haka ma igiya ta kaba misali ne.*

مَآ أَغۡنَىٰ عَنۡهُ مَالُهُۥ وَمَا كَسَبَ ٢

[111:2] Dukiyarsa da duk abin da ya tara, ba za su taimaka masa ba.

سَيَصۡلَىٰ نَارٗا ذَاتَ لَهَبٖ ٣

[111:3] Ya jawo wa kansa wuta mai huruwa.

وَٱمۡرَأَتُهُۥ حَمَّالَةَ ٱلۡحَطَبِ ٤

[111:4] Tare da matarsa wanda ta yi jagorar gallazawa.

فِي جِيدِهَا حَبۡلٞ مِّن مَّسَدِۭ ٥

[111:5] Za tayar da ita (Alqiyamah) da igiyar qaya a wuyanta.